# DALILAI 23 DA SUKA SANYA AKE BUKATAR DOKAR ' YANCIN SAMUN BAYANAI (FOIA) TA 2011

R2K
RIGHT TO KNOW

da taimakon

OPEN SOCIETY INITIATIVE FOR WEST AFRICA

# DALILAI 23 DA SUKA SANYA AKE BUKATAR DOKAR ’YANCIN SAMUN BAYANAI (FOIA) TA 2011

## FOI: DAMAR A SANI: RAYUWARKA TA DOGARA A KAN TA!!!

Dokar ’Yancin Samun Bayanai (FOIA) ta Shekara 2011 ta shafi kowa; ta shafi komai, ta kuma shafi al’amuran rayuwar yau da kullum. Dokar ’Yancin Samun Bayani an kirkiro ta ne don sanin halin da gwamnatoci suke gudanar da harkokin mulki a Najeriya. Dokar na da matukar muhimmanci da amfani ga al’ummarmu, sannan kai-tsaye za ta amfani al’ummar Najeriya. Kuma za ta samar da wata hanya na tsoma hannun jama’a wajen gudanar da harkokin mulki, inda gwamnati da jama’a da kamfanoni masu zaman kansu za su ba da gudunmawarsu, kuma a ci gajiyar hada hannu don tafiyar da kyakkyawar shugabanci mafi gaskiya da rikon amana.

## TA YAYA DOKAR ’YANCIN SAMUN BAYANAI ZA TA TAIMAKA GA INGANTA RAYUWARKA?

* Kowane dan kasa zai samu damar sanin kowane bayani ko adanannun takardu in ban da wadanda aka tsame su da ke hannun gwamnati da kamfanoni masu zaman kansu da suke amfani da kudin gwamnati kan yadda suka kashe kudaden wajen gabatar da ayyukansu,

* Kowane dan kasa na da damar samun bayanan da ya nema a cikin kwanaki bakwai.

* Kowane dan kasa yana da damar sanin yadda ake gudanar da abubuwan da suka shafi lafiya da sauran ayyukan inganta rayuwa da yadda ake saye ko bayar da kwangila da kasafi da gudanar da ayyuka ta hadin-gwiwa tsakanin hukumar gwamnati da kamfanoni masu zaman kansu da bayyana kadarorin ma'aikata gwamnati da sauransu.

* Kowane dan kasa zai iya sanya ido kan halin da ake ciki game da ayyukan gwamnati da yadda suka shafi dukkan vangarori ciki har da tsara harkokin rayuwa da ayyuka da tsare-tsare da kula da lafiyar mata da mata masu juna biyu da sauran harkokin kiwon lafiya da samar da ilimi a matakan farko da shirye-shiryen yaki da fatara da talauci da sauran tsare-tsare.

* Kowane dan kasa zai iya neman inda aka sanya gaba game da yadda ake kashe kudaden da aka kasafta don gyara ko samarwa ko bayar da kudin gudanarwa ga wadansu cibiyoyin gwamnati kamar su asibitoci da hanyoyi da wutar lantarki da ingantaccen ruwan sha da sauransu, a tsakanin al'umma, kuma ya tabbatar an tuhumi mutanen da alhakin rashin tabuka abin a-zo-gani ko gudanar da mummunan aiki.

* Al'umma suna iya kare muhallinsu ta hanyar samun cikakken bayani da ba su damar nuna kin amincewa da ayyuka ko shirye-shiryen da za su haifar da matsala ga muhallinsu da zamantakewarsu.

* Al'umma da 'yan kasa za su iya neman bayani da zai tabbatar musu da ko kudaden da aka fitar don gabatar da ayyuka ga jama'a ko aka zuba musu jari sun yi daidai da ayyukan ko jarin da aka zuba ko akasin hakan.

* Gwamnati da sauran jama'a za su iya sanya idanu kan kason kudin da aka bayar don a gudanar da ayyuka a kasa, su kuma tabbatar da an samu daidaito wajen raba ayyukan bunkasa kasa a sassan kasar nan.

* Majalisa tana da damar neman bayani ko tattara adanannun bayanai da za ta yi amfani da su don gudanar da aikinta na sanya ido yadda ya kamata.

* ’Yan majalisar dokoki za su samu bayani na gaskiya da za su yi amfani da shi wajen tsara dokoki masu kyau, tare da karfafa musu gwiwa su gudanar da aikinsu na tsara doka da sanya ido yadda ya kamata.

* Masu harkokin kasuwanci za su iya auna asara ko ribar da za su samu tare da gudanar da harkokin kasuwancinsu yadda ya kamata, sakamakon yadda za su samu kyakkyawar fahimtar irin Karin zuba jari da yin gasa ko abubuwan da za su kawo faduwa ko riba.

* ’Yan kwangilar da suke neman kwangila za su iya gano ko za a bi ka’ida wurin bayar da wannan kwangila kamar yadda yake kunshe cikin doka da ka’idojin hanyar bayar da kwangila ko a’a.

* Manoma na da damar su samu bayani a kan wace irin gudunmawa ko tallafi za su samu daga gwamnati da ke da nasaba da zuba jari wajen samar da irin shuka da sauran kayan noma, kuma su fahimci a ina aka ajiye kayayyakin kuma don amfanin su wane ne.

* Masu kula da aiwatar da kasafin kudi na da damar bin diddigin inda kudaden suke, kuma nawa ne hakikanin kudin da aka kashe.

* ’Yan jarida da gidajen watsa labarai za su samu damar bayyana rahoton gaskiya; tare da kawar da al’adar yada jita-jita da hada baki da karfafa ilimantarwa da muhawara mai amfani a tsakanin jama’a.

*Masu kula da kudaden tallafi za su samu damar bincike kan bayanan kudaden tallafin da aka bayar don binciken ilimi da sauran cibiyoyin bincike da yadda aka rarraba su.

* Mata ’yan kasuwa za su samu damar sanya ido kan yadda qaramar hukuma ko shugabannin kasuwanni suke amfani da kudin shigar da suka biya da sauran kudaden da ake karba daga wurinsu yau da kullum don tsabtace kasuwa da samar da tsaro da kuma samar da kayayyakin inganta rayuwar ’yan kasuwar.

* Masu tsare-tsare za su iya samun tabbataccen bayanin da za su amfani shi wajen shirya tsare-tsare da auna nasarar shirye-shiryen gwamnati tare da kara inganta su a inda ya zama wajibi.

* Dalibai da Masu Bincike da Manyan Masana za su iya samun ingantaccen bayani na gaskiya da za su yi amfani da shi wajen gabatar da muhimmin bincike.

* Kwararru na iya amfana ta wajen kirkiro ayyukan yi ta fannin gudanar da bayanan gwamnati kuma dokar ’Yancin Samun Bayanai (FOIA) za ta samar da sababbin hanyoyin kudin shiga ga kwararrun masu tsara manufofin gwamnati da masu bincike da masu sasanta rikici da masu binciken kudi da akantoci da lauyoyi da sauransu.

* ’Yan Najeriya za su samu damar zaven wanda ya kwanta musu a rai; sakamako bayanin da zai karfafa su su rika shiga ana damawa da su a harkokin zave.

*Ma’aunan hana cin hanci da rashawa za su samu dauki daga Dokar ta FOIA, sannan Dokar FOIA za ta taimaka wa hukumomin da suke yaki da cin hanci da rashawa wajen yakin da suke yi da cin hanci da rashawar.

* Jama’a za su dada samun yakini da amincewa kan ko masu mulki na aikin da ya dace ga jama’a ko kuwa a’a, idan ba sa yi laifin wane ne.

## BAYANI BABBAN MAKAMI NE, YANZU ZA KA IYA SAMUNSA!!!

Domin karin bayani da kuma samun damar sanin Dokar ’Yancin Samun Bayanai, sai a ziyarci shafin intanet na: www.r2knigeria.org, ko a kira wannan lambar: +234 9-7802227.

Wallafar

R2K RIGHT TO KNOW ...YOUR LIFE DEPENDS ON IT

Da taimakon

OPEN SOCIETY INITIATIVE FOR WEST AFRICA